Alhasan da Alhusain su ne shugabannin matasan 'yan Aljanna

Daga Abu Sa'idu Khudri - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Alhasan da Alhusain su ne shugabannin matasan 'yan Aljanna".

[Ingantacce ne] [Tirmizi da Ahmad sun rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya bada labarin cewa jikokinsa biyu Alhassan da Alhussain 'ya'yan Ali ɗan Abu Ɗalib da Faɗima 'yar Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - kuma Allah Ya yarda da su -, su ne shugabannin wanda ya mutu a falala alhali shi yana saurayi kuma ya shiga aljanna, ko cewa sune shugabannin matasan 'yan aljanna in an cere Annabawa da Khalifofi Masu shiryarwa.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/11169